# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Dan Sarki daga Kogi

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: M. Maillot; Lazarus Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: M. Maillot; Sarah S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**

**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**

**Mataimaki Shugaban kasa Yusuf ya mutu! Duka nutanen Masar suka taya iyalinsa bakin ciki. Allah ya yi amfani da Yusuf mutumin Ibriniyawa**

**domin ya cece kasar daga yunwa. Shi mutum ne mai wayo kuma shugaba ne wanda ake kauna. Yanzu ya tafi.**



Fiye da shekaru dari uku sun riga sun wuce. Mutanen Yusuf, Ibriniyawa, sun riga sun zama zuriya mai karfi a Masar. Sabon Firauna ya fara tsoro watakila Ibriniyawan za su iya juya masa baya su yaudare shi, sai ya mai da su bayi.



**Firauna ya wulakanta Ibriniyawan sosai. Ya tilasta su su gina manyan birane. Amma duk da tsanantawan da yake yi musu, Ibriniyawan sun ci gaba da yaduwa.**



**Wata rana, wani umarni mai ban tsoro ya fito daga Firauna. "Kowane jaririn Ibriniyawan da an haife shi sabo, dole a yar da shi a kogin Nilu." Mugu Firauna ya nace sai ya rage yawan mutanen Ibriniyawa. Har ma da kashe jarirai!**



**“Mene ne za mu yi?” dole wani iyali sun yi wannan tunani. Sai suka yanke shawara su saka jaririnsu a Kogin Nilu. Amma a wani abu kamar kwando suka gyara inda ruwa ba zai iya shiga ba.**



**Yana dauke da kaya mai daraja, dan kwalekwalen - kwandon yana gangarowa.  Ko meye zai faru da dan jaririn?**



**Daga nesa, ‘yar’uwar jaririn na kallon ‘yar kwalekwale na kwando na tafiya a hankali tsakanin ciyawar iwa.**



**Nan da babu zato sai ‘yar Firauna da masu mata hidima suka zo kogin domin wanka. Babu yadda za a boye kwandon. Watakila za su wuce ba su hango kwandon ba.**



**"Oh! Ga kwando. Can, a cikin ciyawar iwa. Ko mene ne a ciki ban sani ba." 'Yar Firauna ta umarci masu mata hidima su je su kawo kwandon. Sa'ad da ta bude shi – jaririn ya fara kuka. "Jaririn Ibriniyawa ne," sarauniyar ta yi ihu.**



“Haya ‘yar bebi.  Kina da kyan gani.”  Watakila ‘yar Firauna ta yi magana da ‘yar bebin kamar yadda ake yi wa wadandan sun yi girma.  Watakila ta yi magana a harshen Masarawa tana ce “Ootchie-kootchie Koo-ums”.



Dole Allah ne ya ba ‘yar’uwar jaririn nan hikima na musamman.  Sai a guje ta je wurin ‘yar Firauna.  “Ko in nema miki macen Ibriniyawa ta lura miki da jaririn?”  “Jeki ki nema,” ta amsa.  A tunaninku wace ce ta je ta kawo?



**“Mama!  Ki Zo da sauri!  Oh, ki yi sauri!”  Watakilya yarinyan ba ta da lokaci ta bayana abin da ke faruwa. Tare, su biyu suka ruga da gudu zuwa wurin.**



A bakin kogin, ‘yar Firauna ta mika jaririn. “Ki yi mini renon jaririn. Zan biya ki. Ki kira shi Musa.” Watakila ma’anar Musa a yaren Masarawa shi ne jaririn-ruwa.



**Haka fa aka mayar da Musa zuwa ga iyayensa da gidansa. Suka koya masa ya kaunaci Allah da mutanen Ibriniyawa. Ba da daddewa ba zai zauna a gidan sarki. Tare da ‘yar Firauna. Allah, wanda ya ceci ransa yana da babban shiri domin jaririn nan Musa.**





# Dan Sarki daga Kogi

## Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

## a na samu a

## Fitowa 2

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**